Wanda ya rantse ya ce: Ni barrantacce ne daga Musulunci, kuma idan maƙaryaci ne, to ya kasance kamar yadda ya faɗa, kuma idan ya kasance mai gaskiya, to ba zai dawo Musulunci ba cikin kwanciyar hankali

Daga Buraidah, Allah ya yarda da shi, ya ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Duk wanda ya rantse ya ce: Ni barrantacce ne daga Musulunci, idan ya kasance makaryaci ne, to ya kasance kamar yadda ya ce, kuma idan ya kasance mai gaskiya, to ba zai dawo Musulunci ba cikin kwanciyar hankali."
[Ingantacce ne] [Al-Nasa'i Ya Rawaito shi - Abu Daud Ya Rawaito shi - Ahmad ne ya rawaito shi]

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/8965